# LABARI DAGA JIHAR
# KADUNA

# TARIHIN JIHAR KADUNA

Jihar Kaduna na daya daga cikin Jihohin Arewacin Najeriya, an samar da Jihar Kaduna a Shekarar 1967 daga Lardin Arewa ta Tsakiya, da ya hada da Jihar Katsina na yanzu.
Iyakokin Jihar Kaduna sun samu ne a shekarar 1987. Itace Jiha ta hudu mafi girma, kuma ta uku mafi yawan al'umma a Kasa, ana yiwa Jihar taken 'Cibiyar Ilimi' a dalilin kafuwar cibiyoyin ilimi masu daraja a fadin Jihar. Kaduna yana nufin 'Crocodile' da harshen turanci. Kamar yadda ya kasance tafkin kogin Kaduna ya tara kada masu yawan gaske a tarihi.

Kaduna ta kasance daya daga cikin tushen wasu al'ummu a nahiyar Afirika, kamar al'ummar Nok. A lokacin mulkin turawan Ingila, Kaduna ta kasance Birnin Lardin Arewacin Najeriya. A kidayar shekarar 2006, Kaduna na da kimanin mutane 760,084. Bunkasar cigaba daga shekarar 2005 yasa yawan jama'ar birnin ya karu a da yakai mutane miliyon 8.9 na shekarar 2021. Tattalin arzikin Jihar ya dogara ne akan noma, musamman na auduga, da kuma gyada.

## BAYANI AKAN SWAG

Stand with a Girl (SWAG) Initiative, kunyiya ce mai hade da jagorori matasa masu rajin daukaka martabar 'ya'ya mata. Don tabbatar da kowa ce yarinya a Nijeriya ta samu damar cika burinta a ko ina take a cikin kasar.

## BAYANI AKAN MURADIN DMS PROJECT

**MANUFA:**

Tabbatar da karin damar samun ingantattun bayanai na lafiyar jima'i da haihuwa a sabis a tsakanin matasa a Najeriya

**MANUFOFI:**

- Habaka fafutukar matasa kan samar da bayanai don tsare-tsare.
- Karfafa gwiwar mahukunta wajen amfani da bayanai don tsare-tsare.
- Fassara bayanan AYSRH a cikin sauki, jan hankali, da kuma tsari mai jan ra'ayin hahukunta wajen tsare-tsare.
- Habaka littattafan labarai na AYSRH don sadar da sakonni kan ilimin hanyoyin kariya daga samun ciki.

## GARGADI

**Wannan aikin almara ne. Sunaye, jarumai, kasuwanci, abubuwan da suka faru da abubuwan da suka faru sune samfuran tunanin marubucin. Duk wani kamanceceniya da ainihin mutane, rayayyu ko matattu, ko abubuwan da suka faru na gaske na faruwa ne kawai.**

**LABARI**


Gari ya waye cikin yanayi na sanyi a Sakandaren Gwamnatin Jihar Kaduna, a wannan yanayi Mrs Laraba ta shiga SS1B domin gabatar da darasi ga dalibai akan Zamantakewar Iyali da Ilimin Kula da Lafiya. Ta fara da bitar jadawalin darasin, sai ta lura wasu daga cikin daliban sunyi biris nutsuwarsu baya tare da ita. Domin dawo da hankulan su, tayi amfani da salon labari domin gabatar da darasin.

**Mrs. Laraba:** “Daga cikin darasin mu na yau, zamu duba labarin wasu 'yan mata guda biyu Esther da Asabe. Za kuji labarin Esther, bayan haka zamu kalli wani dan gajeren bidiyo akan Asabe. "Esther dai ta kasance kamar kowa daga cikin ku dake zaune anan..."




**Esther Bitrus, 'yar shekara 15, ta kasance dalibar SS1 a GSS Sabon Tasha na Karamar Hukumar Chikun. Ta kasance yarinya mai ilimi da hazaka sosai, tana fatan zama malamar makaranta da kuma samun nata iyalin watarana. Tana rayuwa a Sabon Tasha na Jihar Kaduna, tare da mahaifinta, mahaifiyarta da kannenta biyu.**

**Mutanen garin sun kasance masu kyamar ko wane irin tattaunawa akan SRH a tsakanin matasa, suna ganin hakan zaiyi sanadiyyar matasan suna aikata dabi'un da basu dace ba. A dalilin hakan kuwa, dayawa daga cikin 'yan mata da samarin garin basu da wata wayewar ilimin kula da lafiyar su.**



Esther ta hadu da Joseph dan shekara 22, ta kamu da soyayyar sa, a wani lokaci da taje ziyarar gani da ido tare da wasu daliban makarantar su a Kamfanin Taliya da yake aiki a matsayin Dillali. Ta manta jakar makarantar ta a kamfanin, sai ta roki kawarta Jummai da tayi mata rakiya domin su je su dauko.





Da suka koma Kamfanin, sun tarar da Joseph, ya kuma tambaye su cikin raha, ko menene dalilin dawowar su? Sai ko suka kuwa sanar masa. Ya shaida musu cewa ofishin da kayan nasu ke ajiye yana kulle a wannan lokacin. A yayin da Esther da Jummai ke nazarin mafita, ya gano cewa Esther tana son shi. Sai ko yayi alkawarin zai taho mata da jakar gida bayan an tashi daga aiki. Ta kuwa amince da hakan cikin farin ciki.

Joseph ya kai ma Esther jakar ta, ya kuma gaisa da iyayenta, sunyi masa godiya sannan suka bashi yarda bayan sun fahimci sun san iyayen sa, suka kuwa amince zai iya ziyartar su a duk lokacin da ya so hakan. Joseph ya cigaba da zuwa gidan sosai, yana taimakawa Esther da assignments dinta na makaranta. Duk 'yan uwa da kawayen Esther sun fahimci shakuwar abotar su





Watarana, Joseph ya kamu da rashin lafiya har ya kwanta a asibiti. Hakan ya sa baya samun damar ziyartar Esther na tsawon lokaci. Ita kuwa hakan yasa ta shiga damuwa sosai. Ta nemi izinin iyayenta domin taje duba shi. Su ka amince mata. Ta tafi tare da kannenta. Daga zuwan su asibitin sun tarar an sallame Joseph a lokacin. Sun tayashi daukar kayan sa suwa gida. A wannan lokacin ne Esther ta fara zuwa gidan su Joseph, kuma iyalan sa sun ji dadin zuwan ta.

Daga wanan ranar, Esther ta cigaba da ziyartar Joseph kullum tare da kawayenta bayan an tashi a makaranta domin duba shi. Ya kasance yana jin dadin zuwan ta, har ma ta fara ziyartar sa ita kadai. Bayan wani lokaci sun samu kusanci sosai, kuma sunyi jima'i ba tare da kariya ba (Esther tana cikin 4 daga 'yan mata 10 da suka taba yin jima'i ba tare da kariya ba). Iyayenta basu da labari akan faruwar hakan sai kawar ta Jummai wacce ta shaida mata hakan ba wata matsala bane a tsakanin 'yan mata da samari.



**15 - 19**



**4 daga cikin ko wane 'yan mata 10 masu shekara 15-19 a Jihar Kaduna sun yi jima'i ba tare da kayiya ba.**


A lokacin da zasu fara jarabawar Third Term, Esther ta fara rashin lafiya. Tana amai tare da zazzabi ga kuma kasala da take ji a jikinta. Mahaifiyarta ta kai ta asibiti, Likita ya duba ta ya kuma bata wasu gwaji da za a mata, sannan ya bata maganin ciwon jiki kafin a samu sakamakon gwajin. Zazzabin yayi tsanani, hakan yasa bata iya wasu daga cikin jarabawar ta ba.






A lokacin da Esther ta koma karbar sakamakon gwajin, ya nuna Esther ta samu ciki, kuma tana dauke da cutar Hepatitis B (Esther tana cikin 2 daga 'yan mata 10 da sukayi ciki a lokacin kurujiyar su, haka kuma 1 daga cikin 'yan mata 10 basu da ilimi akan wata fasahar kariya daga daukan ciki).

**15 - 19**



**2 a cikin 'yan mata 10 masu shekara 15-19 a Jihar Kaduna sun taba samu ciki a lokacin kuruciyar su**

**15 - 19**



**1 cikin ko wane 'yan mata 10 masu shekara 15-19 a Jihar Kaduna basu da ilimi akan wata fasahar kariya daga samun ciki.**

Esther da mahaifiyarta sun shiga damuwa sosai. Mahaifiyarta tayi fushi da ita har ma ta daina yi mata magana.

Esther da Joseph sunyi shawarin zubar da cikin ta amfani da wani magani da budurwar abokin sa tayi amfani dashi a wani lokaci a baya. Joseph ya tuntubi abokin sa domin samun wannan maganin. Abokin ya fada masa sunan shagon da zai samu wannan maganin, ya kuma je. Esther ta tattauna da Jummai wacce ta bata labarin wani magani da tace yana taimaka wa mata su zubar da ciki. Wata shahararriyar mata ce ke sayar dashi a wannan unguwar ana kiranta 'mama'. Esther ta sha maganin da Jummai da kuma Joseph suka kawo mata ba tare da sanin mahaifiyarta ba.

Da fari, Esther bata ji dadi ba. Ta shiga dakinta domin ta huta. Tayi tunanin yanayin laulayin da take ji na daga tasirin maganin. Cikin dare, Esther ta fara zuban jini tare da ciwon tsananin ciwon mara. Bayan sa'a daya, juriyar ta ya gaza, sai ko ta fara kukan neman taimako. Mahaifiyarta da Mahaifinta suka garzaya dakin cikin hanzari, sai ko suka tarar da Esther a kwance a kasa.



Iyayen suka kai ta asibitin dake kusa, nan take aka shiga da ita Emergency Ward. Sai dai anyi rashin sa'a babu likitan da zai duba ta a lokacin. An samu tazarar lokaci sosai kafin a samu Likita. Zuwa wannan lokacin Esther har ta fita daga hayyacin ta. Da isowar Likitan, yayi bincike kan lafiyar ta, ya kare da zargin yunkurin zubar da ciki tayi.

Sannan ya garzaya da ita theatre domin ceto rayuwarta. Anan akayi ta fafatawa har tsawon sa'a bakwai kafin Likitan yayi nasarar ceton rayuwar ta. Esther tayi barin cikin, sannan mahaifarta ya lalace. Iyayenta sun shiga rudani sosai da suka samu labarin abin da ya faru, suka tuhumi Esther domin ta sanar dasu inda ta samu maganin zubar da ciki.



**Da ya samu labarin Joseph ne sanadi, Mahaifinta ya tafi zuwa gidansu Joseph cikin fushi yana ta zage-zage, kafin yaje ya bada rahoto akan al'amarin ga 'yan sanda wanda suka tafi da Joseph domin tuhumar sa akan zargin sa da akeyi na fyade, duba da shekarun Esther na kuruciya kuma bata da nutsuwar da zatayi zabin da ya dace da ita. Har yanzu ana shari'a a kotu akan lamarin.**




Esther ta shiga dimuwa akan abun da ya faru. Ta shiga kadaici, bata cin abinci sosai, sai yawan sumbatu. Ta yanke hukunci ba zata ci gaba da zuwa makaranta ba domin bata samu damar rubuta wasu jarabawa ba kuma hakan yana nufin sai ta maimaita aji. Ba kawai kwarjinin ta Esther ta rasa ba, har ma mafarkin ta na zama malamar makaranta domin taimakon al'ummar da take, da shirya nata iyalin.



Daliban sun tausaya da jin labarin Esther

**Mrs Laraba:** "Yanzu dai kun ji yanda wannan labarin yake, sannan akwai wani labarin da zaku kalla. Bayan kun gama kallon labarin, zan so ku fada mana bambamcin dake tsakanin labaran guda biyu."

*Ta kunna majigi ta jona da laptop dinta domin haska wani bidiyo.*



**Muryar Mai Sharhi:** Asabe yarinya ce yar shekara 15 tana muradin zama Likita ta farko a garin su. Iyenta talakawa ne a wani karamar kauye da ake kira Gamagira, a Karamar Hukumar Soba. Tare suke da Mahaifiyart domin Mahaifinta ya jima da mutuwa. Faruwar hakan yayi sanadin dawainiyar kula da yaran da dukkan bukatun su akan mahaifiyar su.

Domin cika burinta, Asabe ta kasance tana kawance ne kawai da yara masu hazaka kamarta. Duk da cewa ana zolayarta da akan tsufar da kayan makarantar ta sukayi, hakan bai sa tayi wasa da karatunta a makaranta ba.



**Asabe tana yawan fadama mahaifiyar ta labarin wani mai kudi tsoho Mr. Tanimu a garin su, da yake takura mata a hanyar ta na zuwa makaranta. Yana ce mata wai yana son mu'amala da ita: amma ta fahimci kawai yana so yayi lalata ne da ita. Mahaifiyarta ta bata shawara kada ta sake kula shi, ta dage da karatu kawai.Watarana, Mr Tanimu ya tare Asabe akan hanyarta na komawa gida daga makaranta makar yadda ya saba, ya roke ta akan zai je gidan su ya ziyarci mahaifiyarta, amma Asabe bata amince ayi hakan ba. Ya dage sosai akan bukatar sa, ganin hakan sai taga bata da wani zabi, ta amince, tana fatan mahaifiyarta zata kula da lamarin. Asabe ta barshi a kofa, ta shiga gida da gudu cikin fushi ta fadawa mahaifiyarta domin ta kore shi. Mahaifiyarta bata ji dadin haka ba ta fita cikin fushi domin ta masa kashedi.**





**Mother:** "Fadamin wai me kakeyi a nan?"
**Mr. Tanimu:** "Sannu Ma, nayi tunanin kawo miki ziyara ne, tare da bayyana ra'ayi na akan auren Asabe."
**Mother:** "Nagode. Amma bamu da ra'ayin hakan. Zaka iya tafiya!"
**Mr. Tanimu:** "Dagaske ina sonta, aurenta zanyi. Kuma ina da arzikin da zan iya kula da dukkan bukatun ku."
**Mother:** "Asabe fa karatu takeyi, bata kai aure ba. Sabi da haka kaji da kyau koda auren ne, meye za tayi da tsoho kamar ka. Na roke ka, ka tafi ka bar nan yanzu."
Mahaifiyar Asabe ta tafi ta barshi a gurin bashi da wani zabi sai tafiya kawai.



**Muryar Mai Sharhi**: Bayan sati daya, Mr Tanimu ya tare Asabe yayin da take sauri ta koma gida daga makaranta, ya tambayeta me yasa take sauri zuwa gida haka. Asabe ta fada mishi cewa kaninta ne ba lafiya, tun da safe aka kaishi asibiti, tana sauri domin taje gida ta shirya abinci ta kai asibiti. Mr. Tanimu ya jira ta a daidai gurin da ya saba tare ta. Bayan Asabe ta taho da abincin da ta shirya don zuwa asibiti, ta same shi a tsaye yana jiran ta, ya roke ta don su tafi asibitin tare, ta amince amma kuma bata so hakan ba.



A lokacin da Asabe da Mr. Tanimu suka shiga, suka samu Likita yana bayani akan rashin lafiyar kaninta, cewa kudin jinyar sa zai kai N40000. Mr. Tanimu yace hakan ba matsala bane, zai iya biyan dukkan kudaden. Yace ma Likitan kawai a cigaba da jinyar. Mahaifiyar Asabe bata amince da taimakon sa ba, tace masa ya tafi kawai. Bayan wani lokaci, rashin lafiyar kanin Asabe yayi tsanani, Mahaifiyarta tayi kokarin hada kudaden jinyar amma batayi nasara ba. A wannan yanayin ta zabi ta tura Asabe zuwa gurin Mr. Tanimu. Tayi nazarin hakan ne domin ceton rayuwar danta. Mahaifiyar Asabe ta zauna da ita domin suyi magana.




**Mother:** "Asabe na roke ki, ya kamata ki amince da maganar Mr. Tanimu, ki duba na sayar da zannuwa na masu kyau tare da wasu kayana masu muhimmanci, amma fa ko rabin kudin da ake nema a asibitin bai kai ba. Na samu labarin ya taimaka wa 'yan mata dayawa a wannan kauyen. Dagaske, wata rana Maman Binta ta bani labari ya taimaka musu biyan kudin makarantar Binta har da kudin haya."


**Asabe:** "Nana! wai me kike fadamin haka? Ke ma kin sani mutumin banza ne. Kuma kawaye na sun bani labarin yayi lalata da 'yan mata da yawa ya basu kudi."

**Mother:** "Toh me kike so ki ce? Ai ko yayi lalata dake yanzu, ba matsala bane. Tun da shi yayi alkawari zai aure ki. Ko dai kina so dan'uwan ki ya mutu ne, kuma za mu iya ceton rayuwar sa da wannan kudin? Haba, tausaya halin da dan'uwan ki yake mana. Kawai ki je ki same shi Asabe"



**Muryar Mai Sharhi:** Cikin tsananin damuwa, Asabe ta nemi shawari daga wasu kawayenta domin jin ra'ayinsu. Saratu bata amince da ra'ayin Mahaifiyarta ba, amma Godiya ta ce mata tayi abin da aka umarce ta domin ceto rayuwar kaninta, tace Mahaifiyarta ba zata yafe mata ba idan har tayi sanadin mutuwar kaninta.





**Asabe ta amince ta kuma ziyarci Mr. Tanimu domin tana son kaninta. Kafin tafiyar ta, ta duba wassu darusa a littafin ta lokacin da wani kungiya sa kai sukayi wani taron ilimi a makarantar su akan Ilimin Lafiyar Jima'i da Haihuwa ga Matasa. Anyi musu bayani akan Ilimin Lafiyar Jima'i da Haihuwa sannan aka raba musu kororon roba, ta boye nata a karkashin akwatin ta. Asabe ta dauki kororon robar sai ta kama hanya zuwa gidan tsohon maikudin.**




Bayan ta isa, sunyi hira kadan, sai kuma ya fara shafa jikin ta, ya cire kayan jikin sa. Ya umarceta tayi haka itama. Lokacin da ya zo kusa da ita sai ta cire kororon robar daga cikin jaka ta bashi.

**Mr. Tanimu:** "Meye wannan? Ni fa ban taba amfani da wannan abin tare da wata yarinya da muka yi jima'i tare ba. Rashin amfani dashi yafi bani nishadi"
**Asabe:** "To ba ka san jima'i ba kariya barazana ne gareni na samun cikin da ban shirya masa ba, tare da hatsarin kamuwa da cututtukan da suke yaduwa ta jima'i?"
**Mr. Tanimu:** "Me kike fada ne haka? Ni fa bani da wata matsala. Duk wannan labarun da kika ji karya ne kawai. Ba abin da zai faru."

**Muryar Mai Sharhi:** Asabe tayi kokarin tafiya amma Mr. Tanimu ya tilasta mata ba tare da yin amfani da kororon roba ba. Bayan ya gama, ya jefa mata kudin, ya ce tayi tafiyar ta. (Asabe tana cikin 4 daga 'yan mata 10 da suka taba yin jima'i). Ta koma gida tana kuka, Mahaifiyarta ta rarrasheta tace mata ba abin da zai faru, sannan ta karbe kudaden ta biya kudin jinyar Asibitin.

**15-29**



**4 cikin ‘yan mata 10 masu shekara 15-19 a Jihar Kaduna sun tada yin jima’i**


Rashin nutsuwa da abin da ya faru, ya sa Asabe ta ziyarci cibiyar kula da lafiya, tayi magana da ma'aikacin lafiya daya samu horo akan kula da lafiyar matasa da bukatun su ya kuma bata shawarwari da suka dace, ya kuma tabbatar mata balaifin ta bane. Anyi ma Asabe gwaji akan STI's sannan an bata wani kwayar magani na musamman domin kariya daga daukar ciki.





**Mrs. Laraba:** "Duba da wadannan labarun biyu, wa zai fadamin bambancin da yake cikin rayuwar Esther da Asabe?"

***Yaran maza da mata suka daga hannu, Mrs. Laraba ta zabi yarinyar farko***



**Amina:** "Asabe tana da Ilimin Jima'i da na Haihuwa, hakan ya bata damar kare kanta daga samun ciki bayan anyi mata fyade."

**Mrs Laraba:** "Gaskiya ne! Bari mu ji wasu ra'ayoyin guda biyu."
Josephine: "Asabe ba zatayi nasarar samun maganin kariya daka daukar ciki ba,
da ace babu cibiyar kula da lafiyar matasa a nan unguwar su.

**Mustapha:** "Ina tunanin iyaye suna bukatar fahimtar bayanai akan Ilimin kula da lafiyar Jima'i da Haihuwa ga matasa yana da muhimmanci."

**Mrs Labara:** "Tabbas wannan haka yake! Mun fahimci abubuwa da yawa yau, kuyi nazari akan duk abin da kuka ji da wanda kuka gani, a darasin mu na gaba sai mu tattauna."

# KUNDIN KALMOMI

1) **Zamantakewar Iyali da Ilimin HIV:** shiryayyen tsari na ilimi domin haɓaka samar tabbatattun bayanai na gaskiya, rajin habaka kyawawan halaye, yarda da ra'ayoyi, haɓaka ƙwarewar jure yanayin sauyin rayuwa, tunani, zamantakewa da al'adu na rayuwar ɗan adam.

2) **Lafiyar jima'i na samari da haihuwa:** yanayi na cikakkiyar lafiyar jiki, tunani da zamantakewa ba kawai rashin cuta ko rashin lafiya ba, a cikin dukkan abubuwan da suka shafi tsarin haihuwa na mutane tsakanin shekaru 10 zuwa 19.

3) **Fyade a fuskar Doka:** Fyaɗe a fuskar doka ta dogara ne akan cewa mutum bashi da ikon yarda (amincewa) da yin jima'i, a bisa doka har sai wannan mutum ya kai wani takamaiman shekaru. Doka ta yi umarni da cewa ko da mutum ya amince da yin jima'i da son rai, ba a yarda da hakan ba, don haka ya zama fyade. Wannan yawanci yakan shafi Kananan yara.

# KUNDIN KALMOMI

4) **Kariya daga daukar ciki:** Hanyoyin hana shigar ciki.

5) **Jima'i ba kariya:** Jima'i ba tare da kororon roba ba, ko lokacin da kororon roba ya farke.

6) **Cututtukan da ake yadawa ta hanyar jima'i:** cututtuka ne dake yaduwa ta hanyar jima'i. Kwayoyin cuta na bacteria, virus, ko parasite dake haifar da cututtukan da ake ɗauka ta hanyar jima'i zasu iya yaduwa daga mutum zuwa mutum a cikin jini, maniyyi, ko farji da sauran ruwan jiki.

7) **Mama:** Mother

8) **Nana:** Name of endearment for mother

9) **Sannu Ma:** Well done Ma

# SHIRIN YA SAMU GUDUMAWAR

Jemimah A Menwyah
Usman Garba
Adamu Yusuf Wushishi
Jamila Mohammed
Haliru Ahmad Khalipha
Sim Danjuma Cyrus
Lubabatu Zubairu Gamagira
Mrs Anita
Beribefe Ibule
Jibrin D. Abdullahi
Kayit Michael
Mohammed Aliyu
Tagang Caiphas
Bulus A. Ayesek






# SHAIDAR BAYANAI

**Dukkan bayanan alkaluma da akayi amfani da su wajen ƙirƙirar wannan littafin an samo su ne daga Binciken Kiwon Lafiyar Jama'a ta Najeriya na shekarar 2018.**

# KIRA ZUWA GA MAHUKUNTA

## MA'AIKATUN GWAMNATI

• Fatan bayar da horo na musamman ga ma'aikatan lafiya 255 daga gundumomi 255 akan AYSRH zuwa watan December shekarar 2023.

• Bunkasa horo ga malaman makaranta akan jadawalin darasin Zamantakewar Iyali da Ilimi akan cutar HIV a kowace Karamar Hukuma. Fatan horar da malamai 10 a kowace Karamar Hukuma zuwa watan December shekarar 2023.

• Karfafa AYSRH cikin tsare-tsaren ayyukan kiwon lafiya.

## AL'MMA

• Tabbatar da matasa suna bayar da gudumawa a tsare-tsaren ayyukan kiwon lafiya da ya shafe su kai tsaye a cikin al'umma.

## MUHIMMAN SAKONNI

- Ko wace matashiya tana da damar tayi rayuwa mai nagarta cikin farin ciki.
- Ya dace a bada kariya ga kowace yarinya daga cin zarafi.
- Ya dace a bada kowace yarinya damar samun bayanai akan kula da lafiyarta da na haihuwa.
- A bada kariya ga yara mata daga hatsarin zubar da ciki.
- Iyaye, a kula da lafiyar ta, hakan yana da muhimmanci.
- Lokaci yayi, a koyar da ita akan AYSRH.
- Akan al'amuran AYSRH, a hada hannu domin ceto rayuka.
- Ko wace yarinya tana da iko da jikinta. A bata dama tayi nazari.
- Ni yarinya ce, ina da 'yanci akan zabi na.

# GODIYA TA MUSAMMAN

Wannan littafin labari ya samu goyon bayan Grand Challenges Canada. Grand Challenges Canada na karkashin tallafin gwamnatin kasar Canada kuma an sadaukar da shirin don karfafa ra'ayoyi da ka iya kawo sauyi cikin alumma.

Dukkan bayanai da aka samar cikin wannan littafi hakki ne na Stand with a Girl (SWAG) Initiative masu rajin daukaka martabar 'ya'ya mata. Ba kuma tilas ya zama daidai da ra'ayoyin gamnnatin Canada ko Grand Challenge Canada ba.

KADUNA STATE PRIMARY HEALTH CARE BOARD

ACCESS & EQUITY

STAND WITH A GIRL

SWAG INITIATIVE

Motto: When the society invest in girls, everyone wins

Ministry of Health

Kaduna State Government